**EPISODE 25**

Characters

*Husseini*

*Alhaji Bature*

*Hindatu*

*Hassan*

*Kande*

*Danjuma*

**Scene 1**

*Husseini's shop. Early Afternoon.*

1. **SFX:** **SOUNDS OF ROAD TRAFFIC PASSING B UNDERLAYS SCENE**

2. **ALHAJI:** In wuni Husseini

3. **HUSSEINI:** **(STARTLED)** Alhaji Bature, ah in wuni?!

4. **ALHAJI:** **(LAUGHS)** Hmmm Husseini, kalli fuskarka. Me yasa kake tsoro domin na shigo shagonka eh?

5. **HUSSEINI:** **(UPSET)** Haba Alhaji Bature, ya isa haka! Na san cewa kayi mini taimako can baya, amma wannan cin mutuncin yayi yawa. Yanzu ma kana zagin hankalina ko?

6. **ALHAJI:** **(SOBER)** Husseini, ba haka bane….

7. **HUSSEINI:** **(CUTS IN)** Me yasa kake matsa wa rayuwa na Alhaji? Ko kuma kana son na bar maka *d*an shagon da nake haya ne kuma?

8. **ALHAJI:** Husseini ina..

9. **HUSSEINI:** **(INTERRUPTS)** Kalli nan Alhaji Bature. In ka so kana iya janye duk alkhairin da kake yi mini. Ai komai da iyaka take!

10. **ALHAJI:** Bari na…

11. **HUSSEINI:** **(INTERRUPTS)** A'a! bari na gama magana ta! Allah zai taimake ni na ri*k*e iyali na, kuma zan biya ka duk abun da kake bi na In Sha Allahu.

12. **ALHAJI:** Husseini ba fa*d*a nazo nema ba, nazo ne mu sasanta.

13. **HUSSEINI:** **(SHOCKED)** Ehn?

14. **ALHAJI:** Eh Husseini. Ah kar kayi mamaki mana. Bai dace da na saka matsala tsakanin kai da *d*an-uwanka ba.

15. **HUSSEINI:** Ban gane me kake cewa ba Alhaji

16. **ALHAJI:** **(LAUGHS)** Na zo neman mu shirya, na gaji da zaman maka *k*aya a wuya.

17. **HUSSEINI:** Alhaji, ba wai ban ji dadin haka ba, amma me yasa kayi wannan canjin ra'ayi?

18. **ALHAJI:** Kawai dai ace idanuwa na sun bu*d*e Husseini.

19. **HUSSEINI:** A game da siyasa? Domin na san Hassan bai ja da baya ba, kuma na san bai da niyyar yin haka.

20. **ALHAJI:** Ba game da siyasa bane, wannan ta shafi rayuwata ne.

21. **HUSSEINI:** Toh Alhaji, yaya da naka *d*an takaran?

22. **ALHAJI:** Eh, babu abun da ya canza, zan cigaba da goyon bayansa. Amma ai daman na riga nayi maka al*k*awarin zan taimaka maka, kuma zan cika wannan al*k*awarin.

23. **HUSSEINI:** Allahu Akbar!

24. **ALHAJI:** Alhamdulillah.

25. **HUSSEINI:** Alhaji, wannan lamarin daya sa ka *d*auki wannan canji ba *k*aramin abu bane.

26. **ALHAJI:** Hmm! Kar ma ka fa*d*i!

27. **HUSSEINI**: Hmm! Toh Alhaji, ina yi maka godiya matu*k*a, Allah Ya saka maka da alkhairi.

28. **MUSIC**: <u>**BRIDGE MUSIC**</u>

**Scene 2**

29. **SFX:** **<u>SOUNDS OF ROAD TRAFFIC PASSING B UNDERLAYS SCENE</u>**

30. **HASSAN:** Ina wuni Husseini!!

31. **HUSSEINI:** Hassan! Lallai! Wai-wai-wai, sannu da zuwa!

32. **HASSAN:** **(SURPRISED)** Erm, me yasa kake ta murnar zuwana? Ka ki kayi magana dani ma sati dayawa saboda wannan sha'anin Alhaji Bature.

33. **HUSSEINI:** Haba Hassan! Ina murnar ganinka domin tunda al'amarin ya faru ban yi maka kirki ba.

34. **HASSAN:** Ka manta da wannan. A matsayina da babba, ya kamata na tabbata cewa muna zaman lafiya ko ma menene. Zan iya yin komai domin na taimaka maka.

35. **HUSSEINI:** Ah Hassan, kana da *k*o*k*ari a wannan farnin. Ba don wannan *d*an lokacin ba, ai kai kake kula da iyali na tare da naka.

36. **HASSAN:** Nagode Husseini. Toh dai nazo ne na gaya maka zan sauka daga neman takara, domin ka samu ka cigaba da sana'arka ba tare da wata matsala daga wajen Alhaji Bature.

37. **HUSSEINI:** **(SURPRISED)** Me yasa ka cnaza ra'ayinka kuma Hassan?

38. **HASSAN:** Gwara na samu ha*d*in kai da kwanciyar hankali a cikin iyali na da dan na samu wata matsayin siyasa da zai kawo masifa a cikin iyalin.

39. **HUSSEINI:** Da gaske?

40. **HASSAN:** Eh! Bana son ka rasa hanyar samun kudi a dalili na, musamman ma da sanin yadda ka sha wuya kafin ka fara. Ina son ka samu nasara.

41. **HUSSEINI:** Hassan, ba sai ka sauke takaran ba.

42. **HASSAN:** Na riga na yanke shawara Husseini, kawai ka yarda da shi.

43. **HUSSEINI:** Hassan, Alhaji Bature ya zo *d*azu domin ya gaya mini cewa ya janye maganar ka sauke takaran da kake nema.

44. **HASSAN:** *K*arya ne! Alhaji Bature?! Wannan dai me babbar shago a cikin kasuwa?

45. **HUSSEINI:** Eh, shi Alhaji Bature! Naji murna sosai da cewa zamu koma yadda muke da a cikin iyalinmu.

46. **HASSAN:** **(AMAZED)** Toh me ya faru da shi haka!

47. **HUSSEINI:** Ah, cewa yayi wai wani sha'ani ne daya shafe rayuwarsa, amma bai yi mini bayani ba.

48. **HASSAN:** Nagoda wa Allah cewa abun ya kai *k*arshe.

49. **HUSSEINI:** Alhamdulillahi fa!

50. **HASSAN:** Kila yanzu matayenmu zasu cigaba da hul*d*arsu kamar yadda suka saba.

51. **HUSSEINI:** **(LAUGHING)** Ah ai ka san matata Asabe tana kishi na da yaran. A ganinta tunda ka *k*i kayi yadda na umurce ka, toh fa ka zama ma*k*iyi ne kenan.

52. **HASSAN:** **(LAUGHING)** Eyahh. Sai ka gaya mata cewa nazo na yarda daga baya. **(PAUSES)** *D*an-uwa, naji kewanka fa.

53. **HASSAN:** Nima haka Hassan! Ni ma.

54. **HUSSEINI:** Ka saba bani goyon baya, kai ne ma ka gaya mini batun tazzaran haihuwa, cewa ita ce hanyar samun nasara da moriyar rayuwa.

55. **HASSAN:** Yana da kyau muna kula da junanmu, wannan ya ha*d*u da koya wa junanmu abubuwan da muka koya masu inganci.

56. **HUSSEINI:** Haka ne. yadda nake zama a wannan shago na, bana fasa gaya wa kwastamomi na wai su "Get it Together- Mu ha*d*a kai tare don samar da tazzaran haihuwa."

57. **HASSAN:** **(TEASING)** Hmmm ku kalli *k*ani na fa. Malamin Tazzaran Haihuwa*!*

58. **HUSSEINI:** **(LAUGHING)** Ah Hassan, ina *kok*arin na zama Malan Tazzaran Haihuwa fa. Yadda ka taimaka mini na samu na saka iyali na a hanya mai kyau, haka nima zan taimake wani kuma.

59. **SFX:** **BRIDGE MUSIC**

**Scene 3**

*Alhaji Bature's Residence. Hindatu's room.*

**60. SFX:** **<u>SOUND OF A KNOCK ON A WOODEN DOOR</u>**

**61. SFX:** **<u>DOOR OPENING</u>**

**62. ALHAJI:** Hindatu, Salam alaikum.

**63. HINDATU:** **(HUSKILY)** Wa alaikum was salam Alhaji Bature. Maraba.

**64. ALHAJI:** Haba Hindatu! Me yasa kike kuka har yanzu?

**65. HINDATU:** **(SOBBING LOUDLY)**

**66. ALHAJI:** Hindatu, na ce ya isa mana!

**67. HINDATU:** **(SOBBING, UPSET)** Alhaji, ta yaya zai isa, eh? Ta yaya? Ka gama dani. Ba zai ta*b*a isa ba. **(WAILS)**

**68. ALHAJI:** Haba Hindatu, wato a matsayin maigidanki ba zan iya baki umurni ki *d*auka ba ko? Menene wannan?

**69. HINDATU:** **(SOBBING)** Alhaji, shekara da shekaru ina yi maka biyayya. Ina ta kai ni, eh? Ina Alhaji?

**70. ALHAJI:** **(CARING TONE)** Hindatu…

**71. HINDATU:** **(CUTS IN, ANGRILY, SOBBING)** A'a fa Alhaji. Sai ka gaya mun yanzu! Ina biyayyar da nake yi ta kai ni?

**72. ALHAJI:** Hindatu ki saurare ni tukunna.

**73. HINDATU:** **(HYSTERICAL)** Kana son ka *k*ara cin zali na ko Ahaji?! Mai kuma zaka iya fa*d*i da zai kai wanda ka fa*d*a mini? Bisimillah, ni na gama nawa!

**74. ALHAJI:** **(APOLOGETIC)** Za ace zan iya maido lokaci baya da nayi, na san cewa yaran nan nawa ne.

**75. HINDATU:** Irin wannan zargin ba irin wanda za'a *d*auka da wasa bane, me yasa ka fa*d*i irin wadannan maganganun Alhaji?

**76. ALHAJI:** Na samu wata matsala ne da lafiyar jiki na, amma komai yayi daidai yanzu.

77. **HINDATU:** **(TAKEN ABACK)** Alhaji Bature, wace irin matsala ne wanda zai sa mutum ya zargi matarsa da fasi*k*anci?

78. **ALHAJI:** Hindatu ban kira ki fasi*k*a ba, kawai cewa nayi ki fito da uban yaran.

79. **HINDATU:** Menene bambancin sa da kira na fasi*k*a, eh Alhaji?

80. **ALHAJI:** **(HUMBLE)** Ina neman gafara Hindatu, nayi kuskure. Bai kamata na fa*d*a abun da na fa*d*i ba.

81. **HINDATU:** Babu komai, amma dai Alhaji, ka san abun da addini ya ce game da zargin da kayi mini.

82. **ALHAJI:** Hindatu na riga na baki ha*k*uri. Ina neman gafara.

83. **HINDATU:** Alhaji, nayi ha*k*uri.

84. **ALHAJI:** Nagode. Na gane cewa ni ne da matsala ba ke ba.

85. **HINDATU:** Ko ma menene matsalan, ina fatan zaka magance shi domin mu koma yadda muke da.

86. **ALHAJI:** Haka ne matata. Zan zauna tare da ke anjima mu tattauna akan wannan matsalan da ya shafe lafiyar jiki na. Ina son mu ringa shawara tare domin mu gane ma junanmu, mu kuma samu ha*d*in kai.

87. **HINDATU:** **(HAPPY)** Ah maigida*,* zan so haka kuwa. Bayan duk wa*d*annan shekarun ina son a ce muna da ha*d*in kan junanmu, mu ringa tattaunawa ba tare da wata damuwa ba.

88. **ALHAJI:** Hindatu, ina fatan zaki daina kuka yanzu ko? Bai da kyau. Kalli yadda idanuwanki suka yi ja, suka kumbura.

89. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**Scene 4**

*Kande's Residence. Afternoon.*

90. **SFX:** **<u>SOUND OF A KNOCK ON THE DOOR</u>**

91. **KANDE:** Na'am? Ina zuwa.

92. **SFX:** **<u>SOUND OF DOOR OPENING</u>**

93. **DANJUMA:** Ina yini Gwaggo Kande, kin ce na yi maza na zo.

94. **KANDE:** **(GRUNTS)** Mhm. Ka shigo. Ina son magana tare da kai Danjuma.

95. **SFX:** **<u>SOUND OF DOOR CLOSING</u>**

96. **SFX:** **<u>SOUND OF FOOTSTEPS AND THE CHAIR CREAKING AS BOTH SIT</u>**

97. **DANJUMA:** Gwaggo Kande, ranki a *b*ace yake. Menene ya faru? Hannah na nan lafiya ko?

98. **KANDE:** **(BITTERLY)** Danjuma, ashe kana iya kallo na kayi mini wa*d*annan tambayoyi, kamar baka san komai ba.

99. **DANJUMA:** Gwaggo Kande, na riga na ranste miki cewa ban san komai ba. Kin ma ce kin yarda dani, kuma zaki taimaka mini kiyi wa Hannah magana.

100.**KANDE:** Danjuma, me yasa kayi mini *k*arya akan dangantakarka da Tina?

101.**DANJUMA:** **(CONFUED)** Amma babu komai a tsakani na da wannan yarinyar, da kowanne yarinya ma.

102.**KANDE:** Tsaya na saka maka wani abu. Ka saurara.

103.**SFX:** **<u>SOUND OF PHONE CONVERSATION BEING PLAYED, AS TINA'S VOICE IS HEARD WITH PHONE EFFECTS REPEATING THESE TWO LINES (EPISODE 18 LINE 107, AND EPISODE 23, LINE 9)</u>**

104.**DANJUMA:** Ehn? Subahanallahi, wannan muryar Tina ne!

105.**KANDE:** O-ho! Wato ka ji dai da kunnenka!

106.**DANJUMA:** **(SHOCKED)** Tana hauka ne ko menene?! Tana *k*arya ne! Kai, yarinyar nan muguwa ce fa. Da yadda take *k*arya haka, na tabbata tana iya kisa!

107.**KANDE:** Hmmm Danjuma, kar ka nuna kamar baka sani ba, an kama ka kawai!

**108.DANJUMA:** Gwaggo Kande, na rantse babu abun da ya shiga tsakanin ni da ita. Ban san me take fadi ba, kuma zan iya bayyanawa.

**109.KANDE:** Da gaske?

**110.DANJUMA:** Eh Gwaggo, ko ma menene!

**111.KANDE:** Na gaji da wannan gaba da bayan da ake yi, gaskiya ta yi ta fito kowa ya huta.

**112.DANJUMA:** Gwaggo ina shirye na yi komai da kike bu*k*ata!

**113.KANDE:** Da kyau, ga abun da zamu yi … (FADES OUT)

**114.MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**